*salihai, ina shaidawa babu abin bautawa da gaskiya sai Allah, Kuma ina shaidawa Annabi Muhammadu bawansa ne kuma manzonsa ne"*
sannan ka ce:

"اَللَّهُمَّ صَلِّ عَلَى مُحَمَّدٍ وَعَلَى آلِ مُحَمَّدٍ، كَمَا صَلَّيْتَ عَلَى إِبْرَاهِيمَ وَعَلَى آلِ إِبْرَاهِيمَ، إِنَّكَ حَمِيدٌ مَجِيدٌ. اَللَّهُمَّ بَارِكْ عَلَى مُحَمَّدٍ وَعَلَى آلِ مُحَمَّدٍ كَمَا بَارَكْتَ عَلَى إِبْرَاهِيمَ وَعَلَى آلِ إِبْرَاهِيمَ، إِنَّكَ حَمِيدٌ مَجِيدٌ"

**"Alláhumma salli 'alá Muhammadin wa 'alá áli Muhammad, kamá sallaita 'alá Ibráhíma wa 'alá áli Ibráhím, Innaka Hamídun majíd. Alláhumma bárik 'alá Muhammadin wa 'alá áli Muhammad, kama bárakta 'alá Ibráhíma wa 'alá áli Ibráhím, Innaka Hamídun Majíd"**

*"Ya Allah ka yi salati ga Annabi Muhammadu da mutanan gidansa, kamar yadda ka yi salati ga Annabi Ibrahim da mutanan gidansa, haƙiƙa kai abin godiya ne kuma mai girma ne. Ya Allah ka yi albarka ga Annabi Muhammadu da mutanan gidansa, kamar yadda ka yi albarka ga Annabi Ibrahima da mutanan gidansa, haƙiƙa kai abin godiya ne kuma mai girma ne"*

sannan ka nemi tsari daga abubuwa guda huɗu kana cewa:

"اَللَّهُمَّ إِنِّي أَعُوذُ بِكَ مِنْ عَذَابِ الْقَبْرِ، وَمِنْ عَذَابِ جَهَنَّمَ، وَمِنْ فِتْنَةِ الْمَحْيَى وَالْمَمَاتِ، وَمِنْ شَرِّ فِتْنَةِ الْمَسِيحِ الدَّجَالِ"

**"Alláhumma inní a'úzu bika min 'azábil-ƙabr, wa min 'azábi jahannam, wa min finatil-mahyá wal-mamáti wa min fitnatil-masihid-dajjál"**

*"Ya Allah ina neman tsari daga azabar ƙabari, da azabar wuta, da fitinar rayuwa da ta mutuwa, ina kuma neman tsari da fitinar dujal"*

Daga nan kana da damar da za ka roƙi Allah da abin da ka so kafin sallama kamar:

"اَللَّهُمَّ أَعِنِّي عَلَى ذِكْرِكَ وَشُكْرِكَ وَحُسْنِ عِبَادَتِكَ"

**"Alláhumma a'inní 'alá zikirika wa shukrika wa husni ibádatik"**

*"Ya Allah ka taimake ni akan ambatonka, da gode maka da kyautata bautarka"*

"اَللَّهُمَّ إِنِّي أَسْأَلُكَ الْجَنَّةَ، وَأَعُوذُ بِكَ مِنَ النَّارِ"

**"Alláhumma inní as-alukal-jannata wa a'úzu bika minan-nár"**



*"Ya Allah ina roƙonka aljanna ina neman tsari a wajanka daga wuta"*

(12) Ka yi sallama dama da hagu kana mai cewa a kowanne ɓangare:

"اَلسَّلاَمُ عَلَيْكُمْ وَرَحْمَةُ اللهِ"

**"Assalámu 'alaikum warahmatu-lláh"**

*"Amincin Allah agareku da rahamarsa"*

(13) Idan sallar mai raka'a uku ce kamar *magriba*, ko mai raka'a huɗu kamar *azahar da la'asar da isha*, idan ka karanta tahiya za ka tashi zuwa raka'a ta uku, kana mai dogara akan guiwoyinka (saɓanin sura ta 4) kana mai ɗaga hannayanka (kamar yadda yake a sura ta 1) ka ce:

"اَللَّهُ أَكْبَرُ" **"Alláhu akbar"**

(14) Ka karanta fatiha kawai sannan ka cigaba da sallarka kamar yadda ya gabata, sannan kayi tahiya a ƙarshen raka'a ta uku idan magriba ce, da ƙarshen raka'a ta huɗu a azahar da la'asar da isha, kamar yadda ya gabata a sallah mai raka'a biyu, sannan ka zauna akan Ɗuwawunka na hagu kana mai sanya ƙafarka ta hagu a ƙarƙashin ƙafarka ta dama kana mai shimfiɗa ko kuma ƙafa ƙafarka ta dama a kasa. (za ka iya yin duk wanda kaga dama kamar yadda yake a hoto na 8) sannan ka yi sallama.




KAMAR YADDA YA GABATA KA NUTSU A CIKINTA.

(15) Ya kamata ga musulmi ya kiyaye salloli guda biyar ya rinƙa yinsu a jama'a a cikin masallaci, kar kuma ya rinƙa sakaci da ita don ya zama daga cikin masu babban rabo, in Allah maɗaukaki ya so.

(16) A na so ga kowanne musulmi da musulma su sallaci raka'a goma sha biyu a kowacce rana, a lokacin da suke gida (an fiso ya yita a gida), raka'a biyu kafin sallar asuba, huɗu kafin azahar, biyu bayanta, biyu bayan magriba, biyu bayan isha.

Annabi ﷺ yana cewa: *"Wanda ya yi raka'a goma sha biyu a dare da rana za'a gina masa gida a cikin aljanna"* Muslim ne ya rawaito shi 728. Amma a halin tafiya sai ya bar nafilar azahar da la'asar da isha ya yi ta asuba da witiri kawai.



**(17) Wasu daga cikin kura-kuran wasu masalla'ta':**

1-Riganyar Mamu Limaminsa ko kuma yin aiki tare da shi ya yin da ake yin sallar jam'i

2-Mutum ya dinga ɗaga kansa zuwa sama




## SIFFAR SALLAR JANA'IZA

(1) Ka yi kabbarar harama kana niyyar yin sallah ga mamaci (kana mai ɗaga hannayanka kamar yadda yake a hoto na 1) kana mai cewa:



"اَللَّهُ أَكْبَرُ"

**"Alláhu akbar"**

Ka sanya hannayanka akan ƙirjinka (kamar yadda yake a ɗaya daga cikin hoto na 2)

(2) Ka yi kabbara ta biyu kana mai ɗaga hannayanka kamar yadda ka yi a ta farko kana mai cewa: "اَللَّهُ أَكْبَرُ" **"Alláhu akbar"**

Ka sanya hannayaka akan ƙirjinka, kamar



yadda ka yi a kabbarar farko, sannan ka yi salati ga Annabi ﷺ.

(3) Ka yi kabbara ta uku ka ɗaga hannayanka kana mai cewa: "اَللَّهُ أَكْبَرُ" **"Alláhu akbar"**

Ka sanya hannayaka akan ƙirjinka, kamar yadda ya gabata sannan ka roƙa ma mamaci Allah, da adu'a kamar haka:

"اَللَّهُمَّ اغْفِرْ لِحَيِّنَا وَمَيِّتِنَا وَشَاهِدِنَا وَغَائِبِنَا وَصَغِيرِنَا وَكَبِيرِنَا وَذَكَرِنَا وَأُنْثَانَا، اللَّهُمَّ مَنْ أَحْيَيْتَهُ مِنَّا فَأَحْيِهِ عَلَى الْإِسْلَامِ وَمَنْ تَوَفَّيْتَهُ مِنَّا فَتَوَفَّهُ عَلَى الْإِيمَانِ"

**"Alláhummagfir li-hayyiná wa mayyitiná, wa sháhidiná wa gáibiná, wa sagíriná wa kabíriná, wa zakariná wa unthááná. Alláhumma man ahyaytahu minná fa ahyihi 'alal-islám. Wa man tawaffaitahu minná fa tawaffahu 'alál-ímán"**

*"Ya Allah ka yi gafara ga rayayyunmu da matattunmu da waɗanda suke nan da waɗanda ba sa nan da ƙananamu da manyanmu, da mazanmu da matanmu, Ya Allah wanda ka raya shi a cikinmu ka raya shi akan musulunci wanda ka kashe shi a cikinmu ka kashe ya mai imani"*

(4) Sannan ka yi kabbara ta huɗu kana mai ɗaga hannayanka kana mai cewa:

"اَللَّهُ أَكْبَرُ" **"Alláhu akbar"**

Ka sanya hannayaka akan ƙirjinka, kamar yadda ya gabata, sannan ka yi sallama kana mai cewa: "اَلسَّلاَمُ عَلَيْكُمْ وَرَحْمَةُ اللهِ"

**"Assalámu 'alaikum warahmatu-lláh"**

---

**Manzon Allah ﷺ yace:** *"Wanda ya halarti janaiza har a sallace ta yana da ƙiraɗi, wanda ko ya halarce ta har a bunne ta yanada ƙiraɗi biyu".* Sai akace da shi: Kamar yaya ne ƙiraɗin nan biyu suke? Sai yace: *"Kamar duwatshu guda biyu manya manya".* Bukhari 1325, da muslim 945

**Ya kuma ce:** *"Ku gaggawta da janaiza, in ta kasance ta gari za ku gabatar da ita zuwa ga alhkairi, idan kuma ta kasance wanin haka sharri ne za ku sawke daga kanunku".* Bukhari 1315, da muslim 944

رقم سجل لدى الادارة العامة للبحوث، والتأليف، والترجمة بالأزهر الشريف (17898)





*Allah yana cewa:*

﴿إِنَّ الصَّلَاةَ كَانَتْ عَلَى الْمُؤْمِنِينَ كِتَابًا مَوْقُوتًا﴾ النساء- 103

﴿Haƙiƙa sallah wajiba ce akan muminai a cikin lokaci ƙayyadajje﴾

*Annabi ﷺ yana cewa:*

- *"Wanda ya kiyaye sallah za ta zamar masa haske da hujja da tsira ranar alƙiyama".* Ahmad 6040, Darimi 2721
- *"Tsakanin mutum da shirka da kafurci barin sallah".* Muslim 82
- *"Ku yi sallah kamar yadda ku ka ga ina yi".* Bukari 631

# SIFFAR SALLAR MANZON ALLAH (ﷺ) A TAKAICE




# صفة صلاة النبي ﷺ -باختصار-



باللغة الهوساوية
Da Hausa


بلغات العالم *50 لغة*
غازي بن علي سلطان الداغستاني
المتخرج من الجامعة الإسلامية بالمدينة المنورة
المدينة المنورة +966504352709
1432/2011 +201115587559

الهوساوية

(á)-(í)-(ú): ana nifi da wanan alamar da ke kan wa 'inan haruffan cewa zaa jasu wajan karantawa.
('a): ana nifi da wanan harafi an baki.


(1) Idan za ka yi sallah ga Allah maɗaukaki, ya wajaba agareka ka kasance cikin tsarki cikakke, ka fuskanci alƙibla (ka'aba) da dukkan jikinka ko a ina ka ke daga farkon sallah zuwa ƙarshenta kana mai niyyar yin sallar da ka ke so da zuciyarka wannan ya haɗa da sallar farilla da ta nafila.




(2) Ka yi kabbarar harama (kana mai kallon wajan sujjadarka, kana mai ɗaga hannayanka daura da kafaɗarka ko kusa da kunnuwanka, kamar yadda yake a cikin hoton mai number 1) kana mai cewa:

"اَللَّهُ أَكْبَرُ" **"Alláhu akbar"** *"Allah mai girma"*

(3) Ka sanya hannayanka lokacin da kake a tsaye akan kirjinka, (dama akan hagu) kamar yadda ka gani a ɗaya daga cikin waɗannan hotunan guda 2, sannan ka karanta adduar buɗe sallah:




"سُبْحَانَكَ اللَّهُمَّ وَبِحَمْدِكَ، وَتَبَارَكَ اسْمُكَ، وَتَعَالَى جَدُّكَ، وَلاَ إِلَهَ غَيْرُكَ"

**"Subhánakal-láhumma wa bi-hamdik, wa tabárakasmuk, wa ta'ála jadduk, wa lá iláha gairuk"**

*"Tsarki da godiya gareka suke ya Allah, sunanka ya tsarkaka, girmanka ya daukaka, babu wani abun bautawa da gaskiya sai kai"*

sannan ka ce:

"أَعُوذُ بِاللهِ مِنَ الشَّيْطَانِ الرَّجِيمِ"



**"A'úzu billáhi minash-shaiḍánir-rajím"**

*"Ina neman tsarin Allah daga shaiɗan abin nisantawa daga rahama"*

ka karanta fatiha:

﴿بِسْمِ اللهِ الرَّحْمَنِ الرَّحِيمِ(١) اَلْحَمْدُ للهِ رَبِّ الْعَالَمِينَ(٢) الرَّحْمَنِ الرَّحِيمِ(٣) مَالِكِ يَوْمِ الدِّينِ(٤) إِيَّاكَ نَعْبُدُ وَإِيَّاكَ نَسْتَعِينُ(٥) اهْدِنَا الصِّرَاطَ الْمُسْتَقِيمَ(٦) صِرَاطَ الَّذِينَ أَنْعَمْتَ عَلَيْهِمْ غَيْرِ الْمَغْضُوبِ عَلَيْهِمْ وَلاَ الضَّالِّينَ(٧)﴾ آمين

**﴿Bismilláhir-rahmánir-rahím(1) Alhamdu lilláhi rabbil 'álamín(2) Arrahmánir-rahím(3) Máliki yaumiddín(4) Iyyáka na'abudu wa iyyaka nasta'in(5) Ihdinassiráḍal-mustaƙím(6) Siráḍal-lazína an'amta 'alaihim, gairil magdhúbi 'alaihim walad-dhááliín(7)﴾ Á mín**

**﴿Ina farawa da sunan Allah mai yawan rahama da jinƙai(1) Godiya ta tabbata ga Allah ubangijin talikai(2) mai yawan rahama mai yawan jinƙai(3) mamalakin ranar sakamako(4) kai kaɗai muke bautawa, kuma da gareka kaɗai muke neman taimako(5) shiryar damu zuwa tafarki madaidaici(6) tafarkin waɗanda ka yi musu ni'ima, ba waɗanda ka yi fushi da su ba, ba kuma ɓatattu ba(7)﴾** *"Amin"*

sannan ka karanta abin da ya sawwaƙa na daga alqur'ani

(4) Sannan ka yi ruku'i kana mai ɗaga hannayaka daura da kafaɗunka ko daura da kunnuwanka. Kana mai cewa:

"اَللَّهُ أَكْبَرُ" **"Alláhu akbar"**

Idan za ka yi ruku'u ka daidaita kanka da bayanka, kana mai sanya hannayanka akan guiwoyinka, kana mai buɗa 'yanyatsun hannayanka kamar yadda yake a hoto mai number 3, sannan ka ce sau uku:




"سُبْحَانَ رَبِّيَ الْعَظِيمِ"



**"Subhána Rabbiyal-'Azím"**

*"Tsarki ya tabbata ga ubangijina mai girma"*

(5) Ka ta so da kanka daga ruku'u kana mai ɗaga hannayanka kamar yadda ka gani a hoto, kace:

"سَمِعَ اللَّهُ لِمَنْ حَمِدَهُ"

**"Sami'a-lláhu liman hamidah"**

*"Allah ya amsawa wanda ya gode masa"*

Sannan ka ce bayan ka miƙe:

"رَبَّنَا وَلَكَ الْحَمْدُ، حَمْدًا كَثِيرًا طَيِّبًا مُبَارَكًا فِيهِ"


**"Rabbaná walakalhamd, hamdan kathíran ḍayyibam-mubárakan fíh"**

*"Ya ubangiji gareka godiya take, godiya maiyawa mai tsarki mai albarksa acikinsa"*

(6) Ka yi sujjada kana mai cewa:


"اَللَّهُ أَكْبَرُ" **"Alláhu akbar"**

Ka sanya guiwoyinka a ƙasa kafin hannayanka in hakan ta samu (kamar yadda ka gani a hoto 4.1-4.4) kana mai




fusƙantar da 'yanyatsun hannayanka dana ƙafarka zuwa alƙibla, kana mai haɗa 'yanyatsun kafarka, hannayanka suna fuskantar kafaɗunka ko kuma ka sanya su daura da kunnuwanka, ka nisanta damatsanka da gefanka da cikinka daga barin cinyoyika (idan hakan ba zai cutar da mutane ba), ka raba tsakanin guiwoyinka, (haka hukuncin mace ma yake, saidai za ta takure kanta ta saki ƙafafuwanta ta fuskar dama, Kayi sujjada akan gaɓoɓi guda bakwai akan goshinka da hancinka da tafukan hannayanka da gwuiwoyinka guda biyu da tafin 'yatsun kafarka (kamar yadda ka gani a hoto 5.1-5.4).









Sannan ka ce subbahana rabiyal a'ala sau uku:

"سُبْحَانَ رَبِّيَ الْأَعْلَى"

**"Subhána Rabbiyal a'alá"**

*"Tsarki ya tabbata ga ubangijina maɗaukaki"*

kana da damar da zaka roƙi Allah da abin da kake so a cikin sajadodinka (idan ba ka iya larabci ba, za ka iya yi da yaranka).

(7) Ka taso daga sujjada kana mai cewa:

"اَللَّهُ أَكْبَرُ" **"Alláhu akbar"**

Ka zauna akan kafarka ta hagu kana mai kafa 'yanyatsun kafarka ta dama, ko kuma ka zauna akan dugaduganka, ka ɗora hannayanka akan cinyoyinka ko akan guiwoyinka kamar yadda ka gani a hoto mai number 6, sannan ka ce sau biyu:




"رَبِّ اغْفِرْ لِي" **"Rabbigfirlí"** *"Allah ka gafarta mini"*

(8) Ka yi sujjada ta biyu (kamar yadda yake a hoto 5.1-5.4) kana cewa:

"اَللَّهُ أَكْبَرُ" **"Alláhu akbar"**




sannan ka ce sau uku:

"سُبْحَانَ رَبِّيَ الْأَعْلَى" **"Subhána Rabbiyal a'alá"**

(9) Ka ɗago kanka daga sujjada ka miƙe zuwa raka'a ta biyu kana mai dogara akan guiwarka idan hakan ta samu (ka yi akasin sura ta huɗu) kana mai cewa: "اَللَّهُ أَكْبَرُ" **"Alláhu akbar"**

(10) Ka karanta fatiha da abin da ya sawwaƙa na daga alqur'ani (kana mai ɗora hannayaka akan kirjinka kamar yadda yake a sura ta biyu) sannan ka aikata a cikinta kamar yadda ka aikata a raka'a ta ɗaya.

(11) Idan sallar mai raka'a biyu ce kamar *asuba* da sallar *juma'a* da *idi*, ka zauna bayan ka taso daga sujjada ta biyu (kamar yadda yake a hoto mai number 7.




Sannan ka karanta tahiya:

"التَّحِيَّاتُ لِلَّهِ، وَالصَّلَوَاتُ وَالطَّيِّبَاتُ، اَلسَّلاَمُ عَلَيْكَ أَيُّهَا النَّبِيُّ وَرَحْمَةُ اللهِ وَبَرَكَاتُهُ، اَلسَّلاَمُ عَلَيْنَا وَعَلَى عِبَادِ اللهِ الصَّالِحِينَ، أَشْهَدُ أَنْ لاَ إِلَهَ إِلاَّ اللَّهُ، وَأَشْهَدُ أَنَّ مُحَمَّدًا عَبْدُهُ وَرَسُولُهُ"

**"Attahiyátu li-lláh, wassalawátu waḍḍayyibát, as-salámu 'alaika ayyuhan-nabiyyu warahmatu-lláhi wabarkátuh, as-salámu 'alainá wa 'alá 'ibádi-lláhissálihín, ashhadu allá iláha illa-lláh, wa ashhadu anna Muhammadan 'abduhu wa rasúluh"**

*"Gaisuwoyi sun tabbata ga Allah, salloli da daɗaɗan abubuwa* (daga ayuka da maganganu) *sun tabbata ga Allah, Aminci agareka ya kai wannan Annabi da rahamar Allah da albarkarsa, Aminci agare mu da bayin Allah*